**JUMHURIYYAR MISRA TA LARABAWA** **2٧ Jimada al- Ula, 1443**

**MA'AIKATAR ADDININ MUSULUNCI** **٣١ Disamba, 2021**

(١)

**SRIBATAR LOKUTA DA RASHIN TOZARTAR DA SU**

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **(Ina rantsuwa da zamani; saboda yawan abubuwan da ya ƙunsa** na **ban mamaki da lura. Lallai kowane mutum yana cikin wani nau'i na asara; saboda rinjayar da son zuciya da sha'awa da suka taru suka yi masa yawa. Sai dai ban da waɗanda suka yi imani da Allah, suka kuma aikata ayyuka na gari, suka kuma yi ɗã'a da biyayya, suka kuma yi wa juna wasici da riƙo da gaskiya wajen i'itiƙadi da furuci da aiki, suka kuma yi wa juna wasici da haƙuri akan abubuwa masu wahala da suke bijiro wa duk wani wanda ya yi riƙo da addini, waɗannan kam, su ne masu tsira daga wannan asara, masu kuma babban rabo a duniya da lahira)** [al- Asri: 1-3], Ina shaida cewa lallai babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina kuma shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammad bawan Allah ne kuma Manzonsa, Ya Allah Ubangiji ka ƙara masa tsira da aminci da albarka, shi da alayensa da sahabbansa, da duk wanda ya bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, Bayan haka:

Lallai lokaci yana da muhimmanci mai girma, da ƙima maɗaukakiya a rayuwa ɗan Adam, yana cikin manyan ni'imomin da Allah Maɗaukakin Sarki ya yi masa baiwa da su, Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa: **(Ya kuma hore masu rana da wata suna bibiyan juna tutur; saboda haske da kuma gyara tsirrai da dabbobi, ya kuma hore maku dare saboda ku huta, da rana kuma saboda ku fita nema. Ya samar maku da dukan abubuwan da kuke buƙata a rayuwarku waɗanda kamata ya yi a nema, shi ya ba ku kun nema ko ba ku nema ba, kai idan ma kun yi nufin ƙididdige ni'imomin da Allah ya yi maku, ba za**

**ku taɓa iya ƙididdige na'o'insu ba, balle kuma a matsayinsu na ɗaiɗaiku)** [Ibrahim: 33- 34].

Duk wanda yake yi Alƙur'ani mai girma kallo na tsanaki, zai ga irin yanda ya bai wa lokaci muhimmanci na musamman, inda aka kira surori huɗu cikin surorin Alƙur'ani mai girma da sunan wasu lokuta, waɗannan surori su ne: Suratul Fajri, da Suratul Laili, da Suratud Dhuha, da kuma Suratul Asri, haka ma a wurare da dama Allah Maɗaukakin Sarki ya yi rantsuwa da lokuta mabambanta, Allah mai girma yana cewa: **(Ina rantsuwa da hasken alfijir a lokacin da yake korar duhun dare. Da kuma darare goma da suke sanannu a wurin Allah. Da duk wani abu da yake biyu-biyu da wanda yake tilo a cikin komai)** [al- Fajri: 1 -3], haka ma mai girma da ɗaukaka yana cewa: **(Ina rantsuwa da lokacin da rana ta ɗaukaka (hantsi), aka kuma samu nishaɗi wajen aiki. Da dare, idan komai ya yi shiru, duhunsa kuma ya mamaye komai)** [ad- Dhuha: 1-2], Allah mabuwayi yana cewa: **(Da lokacin Asubahi idan ya yi haske, ya yaye komai)** [al- Mudassir: 34], haka ma Allah mai girma yana cewa: **(Ina rantsuwa da dare a lokacin da duhunsa zai mamaye ko'ina. Da yini, idan haskensa ya keto)** [al- Laili: 1- 2].

Wannan muhimmanci da Alƙur'ani ya bai wa lokaci yana nuna mana muhimmancin da yake da shi ne, da kuma wajbcin amfana da shi da ribatarsa wajen aikata ayyukan alhairi da za su amfani mutum da al'ummarsa, da ma ƙasa baki ɗaya, Allah mai girma yana cewa: **(Ku yi rige- rige wajen aikata alhairai..)** [al- Baƙra: 148], haka ma Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Ka ribaci abubuwa guda biyar kafin wasu abubuwa guda biyar su zo: Samartakarka kafin tsufarka, da lafiyarka kafin rashin lafiyarka, da wadatarka kafin talaucinka,**

**da damarka kafin rashin damarka, da rayuwarka kafin mutuwarka)**. Alhassanul Basriy (Allah ya ƙara masa rahama) yana cewa: **Ya ɗan Adam, kai ɗin ba komai ba ne banda kwanaki, a duk sanda rana ta wuce, to wani sashe naka ne ya wuce**.

Saboda haka dole ne mu tsara lokacinmu, mu kuma amfana da dukan sassansa, mu yi aiki tuƙuru mu fa'idanta da gaba ɗayan rayuwarmu; lallai motsi shi ne yake haifar da motsi, shi kuwa kasala, kasala yake haifarwa, lallai idan aka haɗa kaɗan da kaɗan sai ya zama mai yawa, rayuwar ɗan Adam ba komai ba ce da ta wuce wasu rukunai na zamunna waɗanda su ne suka haɗu suka samar da sassan rayuwa, alhairin Allah ya kai zuwa ga wanda yake cewa: **"Bugun zuciyar mutum yana faɗa masa ne cewa: lallai rayuwa ba ta wuce mintoci da sakwanni ba"**.

Lallai muna ƙara tabbatar da cewa tabbas rayuwar mutum na haƙiƙa ita ce, abubuwan da ya iya samarwa na ilmi, da na tunani, ko wasu abubuwa na binciken ilimi da hasashe, ko wani aiki a aikace, da duk wani abu da zai iya ƙaddamarwa wajen hidimta wa ɗan Adam, ba tare da la'akari da tsawon lokacin da ya rayu ba, wani mawaƙi yana cewa: **"Rayuwar matashi ita ce ambatonsa da ya bari ba tsawon lokacin da ya yi ba.. mutuwarsa kuma ita ce taɓewarsa, ba ranar da aka amshi ransa na kusa ba. Saboda haka, ka raya abin da za a ambace da kyautatawa ka adana shi, da haka sai ya zama ka rayu sau biyu kenan a duniya"**.

Ita albarka a rayuwa ba wai ta taƙaita da tsawon shekaru ba ne kawai, tana zuwa ne daidai da irin abin da mutum ya gabatar, ko ya samar a cikin wannan rayuwar, wanda zai zama hidima ne ga addininsa, ko duniyarsa, ko duniyar mutane, fiyayye a cikin mutane shi ne wanda rayuwarsa ta yi tsawo, kuma aikinsa ya yi

kyau, mafi sharri a cikin mutane kuma shi ne wanda rayuwarsa ta yi tsawo, aikinsa kuma ya yi muni, wanda ya fi alhairi a cikin mutane shi ne wanda ya fi amfanar mutane, lallai an tambayi Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) cewa: Ya Manzon Allah, wane mutum ne a cikin mutane ya fi zama alhairi? Sai (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya ce: **(Wanda rayuwarsa ta yi tsawo, kuma aikinsa ya yi kyau)**, sai aka ce: wane ne kuma ya fi zama sharri a cikin mutane?, sai ya ce: **(Wanda rayuwarsa ta yi tsawo, aikinsa kuma ya yi muni)**, haka ma Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Mutumin da Allah ya fi sonsa a cikin mutane shi ne wanda ya fi amfanar mutane)**.

****

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da aminci su tabbata ga fiyayyen halitta, shugabanmu Annabi Muhammadu da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

Kaman yanda shari'ar Musulunci ta zaburar da mu akan muhimmancin rabitar lokuta, haka ma ta yi mana gargaɗi game da rafkana akansu, da kuma hatsarin tozartar da su, Allah mai girma yana cewa: **(Ya ku muminai, ku ciyar daga cikin dukiyoyin da muka azurta ku, kuna masu gaggawar yin haka tun kafin mutuwa ta zo wa kowane ɗaya daga cikinku, ya yi nadama ya ce: ya Ubangiji ka ɗan jinkirta mini zuwa wani ɗan ƙanƙanin lokaci; domin in yawaita bayar da sadaka, in kuma zamo cikin salihan bayi wajen aikata ayyuka na gari. Lallai Allah ba zai taɓa jinkirta wa wani rai lokacin da ajalinsa ya yi ba, lallai Allah yana da cikakkiyar masaniya game da abin da kuke aikatawa, da kuma shi ne zai saka maku)** [al- Munafiƙun: 10- 11], Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana

cewa: **(Ni'imomi guda mutane da yawa suna asara a cikinsu: lafiya da dama),** haka ma (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Diga- digan bawa ba za su gushe ba a ranar alƙiyama har sai an tambaye shi game da abubuwa huɗu: game da rayuwarsa, akan mene ya ƙarar da ita? Da samartakarsa, akan neme ya tsufar da ita? Da dukiyarsa, ta ina ya same ta, kuma ta ina ya kashe ta? Da iliminsa, mene ya yi da shi?)**, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Ku yi sadaka, kafin lokacin da ba za ku iya yin sadaka ba ya zo).**

A cikin mutane akwai wanda lokaci yake sace shi, idan ma lokacin bai sace shi, shi da kansa ne yake yunƙurin kashe lokacin; saboda yana cikin faraga ce mai kisa da ƙosawa, shi bai yi wani abu na al'amarin addininsa ba, bai kuma gabatar da wani abu na duniyarsa ba, Sayyiduna Abdullahi Bn Mas'ud (Allah ya ƙara yarda da shi) yana cewa: Lallai ina matuƙar ƙin in ga mutumin ba ya aikin komai, shi ba aikin duniya ba, ba kuma aikin lahira ba; alhairin Allah ya kai zuwa ga wanda yake cewa: **"Lallai lokaci shi ne mafi darajar abin da na mayar masa da hankali wajen kiyaye shi, ina kuma ganin cewa shi ne mafi sauƙin abin da yake kuɓuce maka".**

Lallai muna matuƙar buƙatar mu raya lokutanmu da abubuwan da za su amfane mu, su kuma yi wa al'ummarmu da ƙasarmu fa'ida, da haka ne za mu sami nasara, mu cigaba, mu kuma samar da jin daɗin duniya da lahira.

**Ya Allah Ubangiji ina roƙon ka sanya albarka a cikin lokutanmu da rayuwarmu.**